MEDIA RELATIONS UNIT
International Committee of the Red Cross
19, avenue de la Paix
1202 Geneva
Switzerland
Phone: +41 22 730 3443
Fax: +41 22 734 8280
press.gva@icrc.org
http://www.icrc.org

# *ICRC – Labarai, lamba 09/64*

14 Satumba 2018

**Najeriya : A yayin da sa'a 24 ke gabatowa, Kungiyar ICRC tana kira da babban murya cikin gaggawa don sakin ma'aikatan kiwon lafiya da ake garkuwa da su**

Geneva/Abuja (ICRC) - Ƙungiyar Red Kuros ta ƙasa-da-ƙasa (ICRC) tana kira cikin gaggawa ga gwamnatin Najeriya da al'ummomi da ma mutane masu faɗa aji, da su taimaka wajen ganin an sako matan nan masu ƙwazo da aka kama ana kuma garkuwa da su a arewa maso gabashin Najeriya a farkon shekaran nan.

Ɗaukan mataki cikin gaggawa yana da muhimmanci ainun. Kurewan lokaci na iya kasancewar hallaka wata daga cikin ma'aikatan kiwon lafiya cikin sa'o'i 24.

Ga ƙungiyar nan na islama na yanƙin Afirka ta yamma wato ISWAP da ke riƙe da waɗannan mata, muna kira gare ku da ku nuna tausayi. Muna kira da kada ku hallaka wata ma'aikaciyar jinya da bata da laifi; wanda aikin ta kawai shine taimaka wa al'ummomin a arewa maso gabashin Najeriya.

Hawwa Liman ta yi aiki ne a asibitin da ƙungiyar red kuros ta ƙasa-da-ƙasa (ICRC) ke tallafawa a yayin da aka dauke ta a ranar ɗaya ga watan Maris, a yayin da ita kuma Alice Loksha, tayi aiki ne a asibitin da UNICEF take tallafawa.

"Hawwa da Alice ma'aikatan kiwon lafiya ne da suka zaɓi yin aiki don taimaka wa al'ummomin a garin Rann da rikici ya shafa matuka" faɗin Mamadu Sow shugaban gudanarwa na ICRC a yankin tafkin Chadi. "Yawan al'ummar garin ya ninka saboda rikicin, yayin da yawancin ma'aikatan kiwon lafiya suka tsere saboda rikicin. Waɗannan mata suna samar da muhimman aiyukan ceton rayukan dubban masu gudun hijira ne. Abin da kawai suke buƙata a wancan lokacin, shine suyi taimako."

Ma'aikaciya ta uku da aka kama tare da Hawwa da Alice – Ma'aikaciyar ICRC Saifura Husseini Ahmed Khorsa – an hallaka ta a watan satumba. Ƙungiyar mu tana kira ga waɗanda suka aikata wannan, da su nisanci sake aikata wannan mummunan aiki. Leah Sharibu, 'yar makaranta mai shekara 15, ita ma an kama ta ne a garin Dapchi, a wani kame na daban a watan Febrairu. Ita ma waɗannan mutanen ne ke rike da ita, kuma wajibi ne mu yi duk abin da ya kamata, don ganin an sako su ba tare cutarwa ba.

"Muna kira da babban murya a gare ku: ku sako waɗannan mata. Su ma'aikatan kiwon lafiya ne da kuma ƙaramar yarinya matashiya. Ba su cikin wannan fada" faɗin Patricia Danzi, Direktan gudanarwa na ICRC a Afirka. "Ya'yan mu ne kuma 'yan'uwanmu ne, ɗaya daga cikin su uwa ce – mata ne masu yara da suke kula da su da ke da buƙatar koma wa ga iyalan su."

**Don ƙarin bayani, tuntuɓi:**

**Aleksandra Matijevic Mosimann, ICRC Abuja, + 234 903 151 5543 (English)**

**Aliyu Dawobe for Hausa, ICRC Abuja, + 234 802 841 7085 (Hausa)**

**Krista Armstrong, ICRC Geneva, +41 79 217 32 87 (English & French)**

**Jason Straziuso, ICRC Geneva, +41 79 949 35 12 (English)**

**Email press.gva@icrc.org or visit our website: www.icrc.org**

**To preview and download the latest ICRC video footage in broadcast quality, go to www.icrcvideonewsroom.org**